# 3 Yahaya

1 Daga dattijon zuwa ga Gayus, wanda nake
kauna da gaske. 2 Ya kaunatace na, ina addu'a
domin ka samu albarka cikin kowanne al'amari,
da kuma koshin lafiya, kamar yadda ruhun ka
yake lafiya. 3 Na yi farin ciki kwarai sa'adda
wadansu 'yan'uwa suka zo suka ba da shaida
a kan bangaskiyar ka, kamar yadda ka ke bin
gaskiya. 4 Ba abin da ya fi faranta mani rai
kamar in ji yayana suna tafiya cikin gaskiya.
5 Ya kaunatace na, kana aiki da aminci zuwa ga
'yan'uwa da baki, 6 wadanda suka shaida kaunar
ka a gaban ikilisiya. Zai yi kyau ka yi masu
taimako da kyakkyawar salama, ta hanyar da
ta dace da masu ibada, 7 domin sabili da sunan
nan ne suka fito, ba su kuma karbar kome a
hannun al'ummai. 8 Don haka ya kamata mu
karbi irin wadannan mutane, domin mu zama
abokan aiki tare da su a kan gaskiya. 9 Na rubuta
wasika zuwa ga ikilisiya, amma Diyotariffis,
wanda ya fi kowa son girma a cikinsu, bai karbe
mu ba. 10 Saboda haka, idan na zo, zan tuna
masa da irin ayukkan sa, da kuma yadda yake
babbata sunayen mu a wurin jama'a da miyagun
kalmomi. Wannan ma bai ishe shi ba, har
ma yana kin karbar 'yan'uwa. Ya kuma hana
wadanda suke son su yin hakan, harma ya kan
kore su daga ikilisiya. 11 Ya kaunatace na, kada
ka yi koyi da mugun abu, sai dai abu mai kyau.
Dukan wanda yake yin abu mai kyau na Allah

ne; mai aikata mugunta kuma bai san Allah
ba. 12 Dimitiriyas yana da kyakkyawar shaida a
gun kowa har a wurin gaskiyar da kanta. Mu
ma mun shaida shi, ka kuma san shaidar mu
gaskiya ce. 13 Ina da abubuwa dayawa da zan
rubuta maka, amma ban so in rubuta maka su
da alkalami da tawada ba. 14 Ina sa zuciya mu
sadu ba da dadewa ba, sa'annan mu yi magana
ido da ido. 15 Bari salama ta kasance tare da
kai. Abokanmu suna gaishe ka, kuma ka isadda
sakon gaisuwar mu ga sauran abokai da sunayen
su.

# Litafi Mai-tsarki

## The New Testament in the Hausa language of Nigeria

copyright © 2020 Door43 World Missions Community

Language: Hausa

Translation by: Alakirawa, Bayan, Chrispher Ishaya, Dabere, Dacuhus Timothy Danjuma, Danjay, Danjuma Alfred H, Euang Hediza Naohammed, Franklyn Ukazu Udochukwu, Gideon, Gokop, Habibu, James, Kiash Dachung Butus, Lazarus, Nadaki M. Philip, Nenching, Paul, Rebecca, Rev. Ayuba Taiba, Rev. Cain Yusuf Daniel, Rev. Dalhatu Dambo Ayuba, Rev. Dr. Tambanya Yahaya, Rev. Dr. Yakubu Hassan, Rev. Hannatu Samuel Ndberhukwu, Rev. Ibrahim Kassim, Rev. M. Dan'Amarya, Rev. Yakuba Ayuba

Contributor: Dacuhus Timothy Danjuma, Euang Hediza Naohammed, Kiash Dachung Butus, Nadaki M. Philip, Rev. Ayuba Taiba, Rev. Cain Yusuf Daniel, Rev. Dalhatu Dambo Ayuba, Rev. Dr. Tambanya Yahaya, Rev. Dr. Yakubu Hassan, Rev. Hannatu Samuel Ndberhukwu, Rev. Ibrahim Kassim, Rev. M. Dan'Amarya, Rev. Yakuba Ayuba

This translation is made available to you under the terms of the Creative Commons Attribution Share-Alike license 4.0.
You have permission to share and redistribute this Bible translation in any format and to make reasonable revisions and adaptations of this translation, provided that:

- You include the above copyright and source information.
- If you make any changes to the text, you must indicate that you did so in a way that makes it clear that the original licensor is not necessarily endorsing your changes.
- If you redistribute this text, you must distribute your contributions under the same license as the original.

Pictures included with Scriptures and other documents on this site are licensed just for use with those Scriptures and documents. For other uses, please contact the respective copyright owners.
Note that in addition to the rules above, revising and adapting God's Word involves a great responsibility to be true to God's Word. See Revelation 22:18-19.

2020-06-19

---

PDF generated using Haiola and XeLaTeX on 11 Nov 2022 from source files dated 19 Jun 2020

31fd93a8-6c61-5e08-ad99-3312611b0f4b